Godiya ta tabbata ga Allah wanda Ya maida makircinsa zuwa wasiwasi

Daga Dan Abbas - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Wani mutum ya zo gurin Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - sai ya ce: Ya Manzon Allah, lallai dayanmu yana ji aransa - ana bijiro masa da abu - ya zama toka shi ya fi masa da ya fadi maganar, sai ya ce: "Allah ne mafi girma, Allah ne mafi girma, Godiya ta tabbata ga Allah wanda Ya maida makircinsa zuwa wasiwasi".

[Ingantacce ne] [Abu Dawud da Nasa’i a cikin Alkubra]

Wani mutum ya zo wurin Annabi - tsira da amincin Allah su tabbat agare shi - sai ya ce: Ya Manzon Allah, lallai dayanmu yana jin wani al'amari yana bijiro masa a zuciyarsa, saidai ya fade shi abu ne mai girma ne wanda ya kai matakin ace ya zama toka ya fi soyuwa agare shi akan ya fadeta. Sai Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya yi kabbara sau biyu ya godewa Allah da ya mayar da kaidin Shaidan zuwa ga mujarradin wasuwasi.

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/65012